

Akwai wani Ɗanfulani.

Yana shiga gari cin kasuwa.

Ga dutse kan maciji.



A kan hanya Ɗanfulani ya ga maciji.


Ga babban dutse kan maciji.



Maciji ya roƙi Ɗanfulani.

Ya na son a cire dutse.

Ɗanfulani ya yi shakkar cirewa.



Maciji ya ce babu damuwa.

Maciji ya ce Ɗanfulani ya masa rana.

Shi kuma ba zai masa dare ba.




Ɗanfulani ya ɗaga dutse.

Maciji ya fita ƙasan

dutse.

Sai maciji ya ɗaga kai.

Zai ciji Ɗanfulani.




Danfulani ya ce na yi

maka rana.

Yanzu kana son ka yi

mani dare.



Can sai ga kare ya zo.

Danfulani ya mai da zance.

Kare ya ce ga mafita.



Kare ya ce maciji ya

kwanta.

Ɗanfulani ya mayar da

dutse.

Kare ya ce iya gani iya

ƙyalewa.